# TALAKAWA KU TASHI TSAYE!



INSTITUTE OF CHURCH AND SOCIETY

# *TALAKAWA KU TASHI TSAYE*

Zalunci da Yanci cikin Addinin Kirista


Jan H. Boer


**Abubuwan da ke Ciki**


1. GABATARWA 1
2. ZALUNCI DA SAKEWAR ZAMAN JAMA'A 3
3. ZALUNCI DA RASHIN ADALCI 6
   A. Zalunci da Kaddara 6
   B. Zalunci na Masu Ilimi 12
   C. Zalunci na Ma'aikatan Gwamnati 20
4. IKILISIYA: MATAIMAKIN TALAKAWA 24
   A. Cingaba a Aikin Magani 24
   B. Cingaba a Aikin Gona 26
   C. Bukatar Karin Fadakar da Manoma 28



Christian Council of Nigeria

INSTITUTE OF CHURCH AND SOCIETY

Hedkwata:
Oyo Road
P.O. Box 4020
Ibadan, Nigeria

Ofishin Nijeriya ta Arewa:
13, Bukuru Road
P.O. Box 6485
Jos, Nigeria

1987

## GABATARWA

A da dai Bani Isra'ila bayi ne a ƙasar Masar har shekaru ɗari huɗu (400). Daga bisani aka 'yantad da su. Su kuwa suka yi farin ciki ƙwarai. Duk da haka dai zamansu bai yi masu daɗi ba, kuma ba da daɗewa ba suka tsokani Annabi Musa, suka ce, "Don me ka ɗauke mu daga tukwanen nama na ƙasar Masar? Zamanmu ya fi mamu daɗi a can. Yanzu sai wahala muke shä kurum."

A da dai Nijeriya tana ƙarƙashin mulkin wata ƙasa kusan shekara ɗari. Sai kuma aka 'yantad da mu. Zukatanmu suka cika da murnar hangen abubuwa masu kyau a gaba. Yanzu za mu shirya komai namu da kanmu.

Duk da haka yau a cikin ƙasar nan akwai kuka har da hawaye. Waɗansu mutane kuwa suna mamaki har suna tada murya suna tambaya cewa, "Ina amfanin 'yancinmu?" Ai, a wancan zamani komai ya fi sauƙi da araha da jin daɗin rayuwa. Yanzu sai zaluntarmu ake yi kawai. Ga ƙarin kuɗi ko'ina, amma ba a sayen abu kamar shekarun baya. To, ina alkwarai na ƙasa mai jin daɗi, ƙasa mai zubas da madara da zuma -ko dai mai zubas da mai? An sha yi mana alkawarai masu yawa. An yi mana alkawarin 'yanci da na martaba da kuma na kaddara a hannuwanmu. An yi wa ɗamrarru shela ta 'yanci.

A halin da ake ciki a yau dai ana kuka mai zafi a cikin ƙasan nan. Maimakon 'yanci da martaba, sake-saken da aka kawo dai sun dada kara wa talakawa wahalar samun abin zaman gari. Waɗansu mutane kima kuma masu wayo musamman a cikin manyan garuruwa suke cin amfanin dukan sake-saken, amma mazaunan ƙauyuka sun rasa yadda za su bi da masu wayon nan.

An yi taron ma'aikatan ƙungiyoyin inganta zaman ƙauye waɗandanda ke a hannun ikilisiya, musamman daga jihohin arewa. An yi wannan taro a Theological College of Northern Nigeria (TCNN), a Bukuru, Jihar Pilato. Kan maganar taruwar ke nan, "ALHAKIN KIRISTA A CIKIN KYAUTATA ZAMAN KAUYUKA." Mahalartan taron suka dudduba

ayyukansu bisa ga Bisharar Kiristi da kuma abubuwan da suka shafi bukatun mazamnan ƙauyuka.

Nan gaba kadan za a ga taƙaitatun shawarwarin da aka tattauna tare da maganganun da suka bullo daga cikin abubuwan da aka dudduba. Aka tabbatar da waɗansu 'yan zartarwa akan matakin da za a ɗauka a nan gaba, kuma akan taimakon da ake bukata na yin aiki a ƙauyuka yadda za su zama da ma'ana.

An wallafa wannan rahoto don a yi amfani da shi cikin makarantun horad da daliban Littafi Mai Tsarki da kuma wajen horon ma'aikatan ƙungiyoyin ƙyautata zaman ƙauyuka. Kuma an wallafa ne don talakawa da kansu su gane matsayinsu har su san yadda za su tashi su ƙi zaluncin da ake yi masu, su sami 'yancinsu yadda aka yi masu alkawari tun ba mu sami mulkin kanmu ba.

Kwanan baya TEKAN ta bullo da wata takarda kuma ta nuna ra'ayinta na game da tsarin mulkin da zai dace Nijeriya ta ɗauka. Sai ka nemi takardar ka karanta. Za ka ga yadda ra'ayin TEKAN da wanda aka fassarta a wannan takarda ke goyon bayan juna. Ya kamata a karanta su duka tare, a aikata zantattukan da ke cikinsu takarda guda biyu domin talakawa su sami cikakken 'yancinsu. Bari talakawa su tashi da tsayuwar daka, su rabu da tsoro cikin ikon Isa Almasihu.

Jan H. Boer
Jos, Nigeria

## ZALUNCI DA SAKEWAR ZAMAN JAMA'A

Canje-canje masu yawa sun auku a Nijeriya tun samun mulkin kai. Wani lokaci sakewa ta iya zama da amfani ga rayuwar ɗan adam. Sakewa hali ne na rayuwa a nan duniya. A halitta akwai canji akai akai. Canje-canje a ƙasar Nijeriya tun samun mulkin kai sun taɓa harkokin siyasa da na ilimi da na tsimi da kuma a tanadi har ma da na addini. Yawancin canje-canje sun auku domin ƙoƙarin kowa da kowa na cin gaba cikin zaman rayuwar ƙasarmu. Waɗansu canje-canje an yi tsarinsu ne, amma a kashin gaskiya dai yawancin canje-canje ba a yi tsarinsu ba ko kaɗan. Mutane da yawa ba su iya su daidaita zamansu ga sakewar da aka yi cikin hamzari a shekaru 27 da suka wuce ba. Manyan canje-canjen su ne: samun mulkin kai, gwamnatin soja ta danƙa mulki ga farar hula, kakkafa jihohi, faɗaɗa manyan makarantun ilimi, manya ayyukan kwangila, karɓar makarantu da giggina ma'aikatu da masana'antu da hanyoyi da kuma kafa ƙananan hukumomi. Kada kuma a manta da kuɗin mai. Daga baya kuma gwamnatin farar hula ta kasa har sojoji suka sake karɓar mulkin Nijeriya. Kuɗin mai ya ƙare. Kuɗin kayayyaki ya dinga hawa. An rufe wasu kamfanoni. Duk gwamnati da kamfanoni suka sallami ma'aikata masu yawa. Talauci ya ƙaru ko'ina kuma darajar Naira ta faɗi. Yanzu kusan kowa da kowa ya fid da zuciya ga jin daɗin rayuwa, balle talakawa.

Sa'anda aka karɓi makarantu, sai aka cigaba da bada ilimi kyauta ga kowa da kowa. Da farı, wannan ilimi kyauta ce domin kowane ɗalibi. Ba'a iya bayyana ya zama haka gaba daya ba. Dole ne ɗalibai su sayi littattafansu da rigunan makaranta, su kuma ɗauki kujerunsu ko tabarmansu zuwa makaranta. Tun sa'anda aka karɓi makarantu daga kungiyoyin addini yara ba su iya cin gaba da samun koyarwar addini ba, sai sa'anda iyayensu da shugabannin ikilisiya suka ɗaukar wa kansu cewa ya kamata su matsa domin a tanadi hanyar koyarda addini ga 'ya'yansu. Saboda haka a halin da ake ciki a yanzu yara da yawa ba su sami koyarwar addini ba.

Yanzu tsadar kayayyaki ta shafi kowa da kowa a Nijeriya. Tsadar abinci da tsadar kayayyyakin gine-gine da waɗansu kayayyaki--duk waɗannan sun jawo wahala ga talakawa ƙwarai da gaske, wato su waɗanda suka fi masu dukiya yawa. Talakawa sun fi kowa yawa, amma ba su da bakin magana. Masu magana su ne attajirai da 'yan siyasa da sojoji da masu digiri. Gwamnati na kasa kunne garesu. Ko loton da ake shawara batun talakawa za a yi ne da waɗansu manya, ba da talakawa su kansu ba. An rena su. Wai ba su gane komai ba. Bugu da ƙari kullum su masu magana na so gwamnati ta sake dudduba matakan albashinsu akai akai. Dan kasuwa mai arziki yana daɗa ƙaruwa da arzikinsa a lokacin da ake ƙara yanke wa manomi ribarsa har ba shi da wata riba ko kaɗan. Ai, manomi ba shi da albashi. Shi yana dogara ga aikin hannuwansa mai wuya domin ya biya bukatarsa.

Manomi a ƙauye dai, ai, yana ci da ƙarfinsa ne kurum. Muhimman bukatun da suka zama wajibi ga ɗan adam manomi ba ya samunsu. Shi dai yakan noma ɗan yankin filinsa, ya kuma shuka, sa'annan ya yi ta jira da hanƙuri har hatsin ya yi girma ya kai lokacin girbi. Bayan girbin kuwa babu wata daidaitacciyar hanyar a gareshi ta sayar da amfaninsa ga mazaunan gari a kuɗin da zai biya bukatarsa, wato tasa bukata da ta matarsa duk da ta 'ya'yansa har zuwa kaka ta gaba. Ba damar ajiyar 'yan kuɗi.

Mai yiwuwa ne kuma da rani mutanen ƙauye za su yi tafiya mai nisan gaske domin neman ruwan sha mai tsabta. Ba wutar lantarki balle ma injin sussukar hatsi. Kauyuka da dama sun rasa hanyoyin da motoci za su bi don kwasar amfanin gonarsu zuwa kasuwa.

Cin gaban al'umma ba cin gaban kayan aiki ne kaɗai ba. Duk da haka dai ana bukatar kayan aiki domin taimakawa cikin cin gabansu. Bukatu don cingaba sun yi yawa. Ga waɗansu bukatun:

—hanyar mota don kai amfanin gona kasuwa.

—ilimi na koyad da samari yadda za su yi zamansu da kuma su kyautata ƙauyensu.

—hanyar tattalin arziki wadda za ta rarraba wadatar al'umma domin kada kowa ya yi zaman talauci.

—injuna don rage wahalar aiki kamar su tirakta na haya daga hannun gwamnati. Bisa ga shiri na yanzu sai manyan manoma da masu bada toshiya su kaɗai ne akan kai masu irin wannan kayan aiki. Da ƙyar talaka zai sami amfanin irin wannan kayan gwamnati.

—hanyar ajiya a banki, wato bankin da aka kafa don taimakon jama'a musamman, ba don ya azurtad da masu bankin ba.

—likitoci da sauran masu aikin magani waɗanda za su zauna a inda yawancin mutane suke, wato a ƙauyuka, ba a cikin birane kaɗai ba.

—takin zamani wanda gwamnati ke kawowa don amfanin manoma duka, amma da ƙyar manoma ke samu sai dai da kuɗin toshi ko kuwa a bakin ƙasuwa da kuɗi fiye da yadda ya kamata.

Nijeriya kafin samun mulkin kai ba Nijeriya ta yau ba ce. Ko da shi ke kamannin birane da ƙauyuka sun sake, amma dangantakar da ke tsakanin jama'a ta sukurkuce. Saboda haka mat-sayin da ke tsakanin masu arziki da talakawa sai ƙara nisa yake yi. Wannan mummunan bambanci tsakanin masu arziki da suke 'yan kima da matalauta zambar dubbai dole ne a yi maganin wannan domin a bayar da cikakkiyar daraja ga dukan 'yan Nijeriya. Manufar samun mulkin kai kuwa ita ce a kawo wa dukan 'yan kasa wadataccen zaman rayuwa. To, amma ina?

TAMBAYOYI:

1. Ko ana koyad da addininka cikin makaranta a kauyenku? In babu, me ya sa? Wa ya hana? Sai a yi shawara yadda za a gyara wannan matasala da kuma a yi aiki da

shawarar da aka yi. Albashin malamin fa? Akwai ko babu? In babu ko ana biyan albashin malamin wani addini?

2. Wane ne ya fi samun abin zaman gari a ƙauyenku — manoma ko kuwa ma'aikatan gwamnati? Ana biyansu da kuɗin wa? Wa ya fi shan wuya a fuskar aiki?
3. Me ya fi kawo damuwa a kauyenku? Rashin hanya ko kuwa fosta ofis ko yaya? Bari a yi shawara don a san bukatar da kuma batun yadda za a iya biya wannan bukata. Me ku da danku za ku iya yi?

## ZALUNCI DA RASHIN ADALCI

Ana iya gane dalilai dabam dabam na shan wahalar talakawan ƙauyuka. Za mu bayyana guda uku a cikinsu a taƙaice tare da misalai da za su goyi bayansu. Dalilai guda uku din nan da za mu ambaɗta mu kuma yi magana akai su ne:

1. Akan mai da kowace hasara ƙaddara, ba abin yi, ba magani.
2. Masu ilimi su kan kwace amfanin talakawa ta wurin wayonsu da matsayinsu.
3. Gwamnati ta kafa ayyuka dabam dabam don taimakon talakawa, amma sai ka ce an kafa su ne don a zalunci talakawa. Talakawa ba su samun amfaninsu yadda ya kamata.

Za mu yi maganar waɗannan dalilai guda uku bi da bi, amma sai a gane cewa tushen dalilan shi ne na farkon, wato batun ƙaddara. Sauran dalilan guda biyu suna goyon bayan na farkon nan.

### A. AKAN MAI DA KOWACE HASARA KADDARA NE BA ABIN YI.

Talakawa sun sani cewa ana cutarsu, amma ya yi musu wuya su buɗe bakinsu su faɗi abin da ya dame su, balle su rubuta. Akwai wuyar yin magana a fili saboda tunanin ƙaddara da ke a

zuciya ya hana ƙarfi da iko, ba abin yi. Ana tunani cewa, "Allah ne ya nufi haka" ko kuwa "Haka zaman duniya yake, sai haƙuri." Har ma Kirista sun manta da zancen Isa Almasihu da ya ce Allah ne

"ya aiko ni in yi shelar saki ga ɗaurarru.
da kuma buɗe wa makafi ido,
in kuma 'yanta waɗanda ke danne..." (Luka 4:18).

Ga waɗansu misalai akan abubuwanda suke damun talakwa, inda talakawan swa iya ɗaukar wani mataki domin su canja matsayinsu, amma ba su yi ba. Tunanin ƙaddara wanda ke a zukatansu ya hana su.

MISALI 1. Wani manomi ya yi ƙoƙarin ya sami takin zamanin da gwamnati ta kawo domin taimakon manoma a ofishin malamin gona, amma ƙoƙarinsu duk ya zama a banza. Sai ya roƙi pasto nasu. Ta wurin taimakon abokansa masu ilimi sai fasto din ya sami takin ba da wata wahala kuma ba. Daga baya manomin ya ce, "Yaushe ne za mu sami 'yanci daga mulkin mallaka da mutanenmu suke yi mana?" Ko da shi ke wannan zalunci ya shafi yawancin manoma, amma a halin da ake ciki da ƙyar za a sami manomin da zai yi tunanin yin wani abu akai. Tunanin ƙaddara da tsoro sun hana shi.

TAMBAYA: Mai yiwuwa ne ya yi wuya mutum daya ya yi maganin wannan damuwa, amma bari ƙungiyar manoma a ƙauyenku ta yi shawara. In ba irin wannan ƙungiyar, ya yiwu a yi shawara cikin ikilisiyar da ke a ƙauyenku. Ba dama a je wajen ofishin Baturen Gona a yi magana, a nuna masa cewa an gaji da wannan hali? Me ya hana? To, sai a yi shawara.

MISALI 2. Akwai hanyoyi da yawa da 'yan kasuwa masu wayo ke bi don su sami takin zamani daga gwamnati ta hanyoyi ƙetare doka, galibinsu ta hanyar toshiyar baki. Sa'anan su sayar ma manoma da tsada ko kuwa da sharadin za su sami sayen amfanin gonarsu da araha ƙwarai da gaske. Tun da shi ke yawancin manoma masu neman takin zamani ne "ido a rufe," domin

haka suka yarda da irin waɗannan shirye-shiryen. Saboda tunanin ƙaddara da tsoro da ido a rufe wajen talakawa, sukan shiga tarkon nan ba tare da su attajiran nan da ma'aikatan gwamnati sun sha wahala akansu ba. Talakawan sun zama abin-ci a sauƙaƙƙe a garesu.

Mun kawo misalai guda biyu kurum da muka gani daga misalai masu yawa da mutane ke aikatawa cikin kasuwanci da ayyukan gwamnati domin ta wurin son kazamtar riba suka zambaci talakawa.

TAMBAYA: WANNAN DAIDAI NE KUWA? Dole ne manoma su ci gaba da haƙuri da wannan wulakanci? Ko ƙungiyarku ko ikilisiyarku tana da wata dabara? A yi shawara. Mai yiwuwa ne waɗansu daga cikin aikin wulakancin nan memba ne na ikilisiyarka. In haka ne a tuna da hanyar da Isa Almasihu da kansa ya nuna mamu mu bi cikin Mat. 18:15-20. In su mazumbata na wani addini ne, sai ku tuna cewa in kun dinga jin tsoronsu za su cigaba da halin zamba. Amma in sun gane cewa ba kwa jin tsoronsu yanzu kuma, kun tashi don neman 'yancinku, su ne za su fara jin tsoronku.

Ban da Luka 4:18, sai kuma a tuna da Wakar Maryamu uwar Isa Almasihu a Luka 1:51-53 inda aka karanta batun ayyukan da shi Almasihu zai aikata cewa:

Manyan ayyuka da ya yi,
Masu girmankai, su da dabarbarunsu ya warwatsa.
Ya firfitar da sarakuna a sarauta,
Ya daukaka ƙaskantattu.
Mayunwata ya ƙosar da abubuwan alheri,
Mawadata kuwa ya saleme su hannu wofi.

MISALI 3. Wata rana da tsakar dare wani pasto ya je asibiti. A bakin ƙofar asibitin ya iske wata tsohuwa a kwance akan daɓen siminti. Da gangan aka ƙi kula da ita. Ta ce ta rase wan-da zai taimake ta ya jawo hankalin masu jinya zuwa wurinta.

Pasto ya kirawo wani mai jinya wanda ya roƙe shi gafara da cewa, "Ai, da na sani cewa akwai dangantaka tsakaninta da kai da na kula da ita!" WATO MACE MARAR MATAIMAKI, BA TA ISA A KULA DA ITA BA?

TAMBAYA: Rashin kula irin wannan yana faruwa kowane lokaci a asibitoccinmu da kuma a ƙanƙanan ɗakunan magani a ƙauyyuka. Ina abin yi ko kuwa ina maganinsa? Za a bar su ma'aikata masu jinya, wato su waɗanda aka ɗauke su don su taimake mu a jiyya waɗanda kuma akan biya su daga cikin kuɗin jama'a cikin wannan hali saboda tunanin ƙaddara da tsoro da ke a zukatanmu? Haba jama'a! A tuna da maganar Isa Almasihu da ta Maryamu, a yi aiki da su maganganunsu cikin sunan Allah.

MISALI 4. A wani kauye wanda yake da makarantar framari yawancin malamai daga waɗansu wurare suka zo, ba 'yan garin ba. Ba su damu da aikin koyarwarsu yadda ya kamata ba. Saboda haka yara kima ne kurum suka ci jarrabawa zuwa waɗansu makarantu. Iyaye suka yi ta yin gunaguni da kuma yawan mita a tsakaninsu, amma ba wanda ya ɗauki wani mataki na ganin an gyara lamarin. Wani ya shawarci wani muhimmin mutum daga cikin iyayen cewa ya tara iyayyen yaran domin su shawarta abin da za su yi. Za su iya yin magana da shugaban makaranta ko kuwa da malaman duka. Ya yiwu ma su aika da wakilansu ga ofishin Hukumar Ilimi a garinsu. Al'amarin bai yi ba domin mutumin ya amsa cewa gwamnati ba ta ba su izinin yin haka ba. Wanda ya ba da shawara ya amsa cewa Allah ne ya ba iyaye nawaya ko alhakin yaransu. Kuma gwamnati tana biyan malamai albashinsu, amma ba su cika aikinsu ba. Saboda haka iyaye na da bakin magana. Amma ba abin da aka yi, sai gunaguni.

TAMBAYA: Idan da irin wannan damuwa a wajenku, wace hanya ce ya kamata a bi? Gaskiya ne kuwa iyaye ba su da bakin magana cikin zancen nan? An ɗauke su

malaman don aikin koyarwa ko kuwa don su karɓi albashi kawai? Ana biyansu kuma da kuɗin wa? Tsoro da tunanin ƙaddara da ke cikin zukatan iyayen ba zai taimaki kowa ba, sai dai su malaman ke jin daɗin irin wannan tsoro. Mai yiwuwa ne wasu malaman Kirista ne. To, sai a bi matakan Mat. 18.

MISALI 5. An taimaka wani gari da ruwan famfo da ake jawo ruwa daga wani kogi wajen mil 20 da garin. Tashar da ake jawo ruwan tana wani ƙauye wanda aka ba bakin famfo daya tak domin dukan jama'ar ƙauyen. Ba su samun ruwan famfo akai akai. Domin haka duk lokacin da aka sami ruwa, sai mutanen ƙauyen su tattaru kewaye da bakin famfon, kowa na kokawar samun bokiti ɗaya na ruwa kafin a rufe ruwan kuma. A da dai suna diban ruwa da yawa daga kogin, amma yanzu an sa waya an kewaye kogin, babu dama a debo ruwa daga kogin. Ga shi kuma bakin famfo ɗaya ne ƙurum. Wannan al'amari ya jawo wa mutanen ƙauyen muhawara da kuma fada da juna. Zaman jin daɗin jama'a ya lalace kwarai da gaske. Duk da koke-kokensu zuwan wurin hukumar ruwa domin a ƙara masu bakin famfo ba'a kula ba. A ƙauyen komain ya zama barkatai.

TAMBAYA: Sai ka ce mutanen nan sun riga sun yi ƙoƙari ta wajen kai kukansu ga hukumar ruwa na garin, amma ba a ji su ba. To, inda wannan ke faruwa ba wani wurin da za a kai kukan ne? Ko ya yiwu mutanen ƙauyen duk baki ɗaya su je wurin hukumar a matsa su har a kwana a kofarsu? Ba wai da zub da jini ko wani abu haka ba fa! A'a. Sai dai a nuna masu cewa an rabu da tsoron banza. A na neman 'yancin da ke cikin Tsarin Mulkin Nijeriya.

MISALI 6. A wani ƙauye ana tsarin gini ɗakin magani domin amfanin dukan jama'a, amma tare da wani kuɗin gwamnati ba tun da shi ke za su haɗa kai da shirin aikin kiwon lafiya da asibitin ikilisiya ke tafiyar da shi. Ana bukatar izinin wani hakimi wanda ke da zamansa a wani ƙauye wajen kilomita biyu

daga wurin. Da shi ke hakimin ya ƙi ba da izini ya hana su hanyar samun taimakon nan wanda jama'a ke bukata. Ba wani dalili kuma sai dai kishi ko kuwa hamayya ta sha'anin zaman jama'a. An bar batun haka, ba aikin magani a wurin har a yau.

TAMBAYA: Me ya kamata mutanen ƙauyen su yi? Ko su bari kawai? Hakimin ke da iko ya hana jama'a ɓukatarsu? Don me aka nada masu hakimi: don ya hana masu bukatunsu ko kuwa ya taya su biyan bukatunsu? Me ya sa har yanzu ba ɗakin magani a wurin? Ba domin jama'a na tsoro ba? Irin tsoron masu daidai ne kuwa? Me Isa Almasihu ya fadi game da irin wannan zamba? To, ina abin yi, jama'a?

MISALI 7. Wani hakimi ya umurci mutanen wani ƙauye cewa su gusa kurkusa da wata sabuwar hanya. Sa'anda mutanen suka tsai da shawararsu cewa sun fi so su zauna a inda suke, sai hakimin ya aika da mutanensa suka ƙone ƙauyen ƙurmus! Mazaunan wurin suka tashi suka gina sabon ƙauyensu a inda hakimi ke so, amma ba wanda ya buɗe bakinsa ya yi magana. Hakimin kuwa yana nan da mugun halinsa har a yau.

TAMBAYA: Me ya kamata mutanen ƙauyen su yi? Su bar maganar haka kawai? Da mutanen ƙauyen nan sun ji maganar Isa Almasihu a Luka 4:18 da kuma Waƙar Maryamu a Luka 1:51-53 da sun bar magana haka? Addinin Kirista ya hana neman 'yanci? Kiristi ya yarda da tsoron banza? Ya yarda da zamba? Ya ce a yi hankuri kurum?

MISALI 8. Sa'ad da aka soma Operation Feed the Nation (Shirin Wadata ƙasa da Abinci) aka kafa kwamitin aikin a kowane wuri a ƙasar Nijeriya. A wani wuri aka kafa kwamiti na manoma wajen 25 da kuma aka sa ranar taron kwamitin. Da lokacin taron ya kewayo kuma sai yawancin manoman suka taru daidai lokacin a ƙofar hakiminsu. Amma fa hakimin bai zo ba ana ta jiransa har wajen sa'a ɗaya da minti 30. Daga baya ya

fito tare da wani ''babban mutum'' daga babban birnin jiharsu. Shi baƙon na wata kabila ne da ke mulki kama karya, wanda kuma ta wurin tafiyarsa da babbar rigarsa kowa ya sani yana son manoman nan su girmama shi, su darajanta shi kuma. Hakimin ya gaya ma ɗaya daga cikin manoman cewa su yi hanƙuri, amma zai zo bayan ''babban baƙon'' ya koma garinsu. An gaya ma hakimin cewa ko da ɓakon zai yi jiransu ba za a rage masa albashinsa ba, amma su manoma suka bar nasu aiki da kuma ba wanda zai ɗauki nauyin nasu lokaci. Su kuwa suka bar gonakinsu domin Operation Feed the Nation! Amma hakimin ya rasa yadda zai yi, sai ya bi ''babban baƙonsa.'' Daya daga cikin su manoman nan ya ba da shawara cewa ya kamata su tashi duka su koma gida, amma ba a ji shi ba. Kowa ya yi biyayya marar ma'ana ga hakimin, ana ta jira. A gaskiya dai, wannan raini ne sosai ga manoman nan.

TAMBAYA: A ganinka irin wannan biyayya daidai ce kuwa? Me kuka gani: shi mai ba da shawara cewa su koma gida daidai ne ko babu? Irin hanƙurin da hakimin ya ba jama'arsa kuma daidai ne? Me ya sa shi bai ba su goyon baya ba?

## 8. ZALUNCIN DA MASU ILIMIN ZAMANI DA KUMA MASU WAYO KE YI.

Domin baiwar iliminsu na zamani, gwamnati ta sa waɗansu mutane a babban matsayin da za a amince da su, su bauta wa jama'a. Amma kaito! Waɗannan masu muƙamin rikon amanar jama'a sau da yawa sukan yi amfani da matsayinsu domin su tara ma kansu dukiya ta kowace hanyar da iliminsu ya koya masu. Ya-yiwu a ce zaluncin da waɗannan suke yi wa 'yanuwansu talakawa ya fi danniyar da Turawan mulkin mallaka suka yi. Masu ilimi na zamani cikin jaridu da kuma cikin littattafansu suke yi ma Turawan mulki na da da kuma na yau sharri da cewa ta wajen wayonsu ne suke yi mamu danniya har wa yau.

Gaskiyarsu kuwa. Amma fa da alama su masu ilimin sukan nanata danniyar da waɗansu Turawa ke yi mana don kada a ga irin danniya da zaluncin da su da kansu sukan yi ma 'yanuwansu talakawa. A lokacin da ake yi wa mutane na wajen sharri da babbar murya wadda dole ne kowa ya ji, su masu sharrin ke yin tsarin kansu su fitar da ribar da suka samu ta wajen hanyar wayonsu su yi ajiya cikin banki a nan Nijeriya ko na ƙasashen waje.

MISALI 1: Hukumar Ilimi tare da makarantu da jami'o'inmu suka fi sauran hukumomi da ayyuka a Nijeriya tanadin danniya. Kowa ya ɗauka cewa dalilin samun ilimi na farko shi ne mutum ya tara ma kansa dukiya. Gaskiya ce kuwa loto-loto wani mai ilimin zai ji daɗin baki da ya shafi maganganun amana da na alhaki da na hidima, amma yawancin lokaci waɗannan masu daɗin baki mutane ne waɗanda suka riga suka ci nasara suna tafiya cikin motici mafiya tsada. Kowa da kowa ya sani cewa ilimi na zamani hanya ce ta samun iko. Ko a wajen Kirista ma haka akan ɗauka har wata makarantar sekandari ta sa wannan a kirarinta, wato "Knowledge is Power," ko kuwa "Ilimi iko ne." Mutanen da su ke samun digiri daga jami'o'inmu ana tanada masu dukan kayayyakin da suke bukata domin su ci amfanin jahilai. Kuma yawancin mutane sun yarda ita ce manufar ilimin zamaninmu. Mutane kima da suka ƙi su hada kai a cikin wannan mugun hali ana tsananta masu. Yawancin Kirista ma na goyon baya; wadansu da ƙyar suka bambanta cikin wannan hali.

> TAMBAYA: Kai, mai karatu, idan kana cikin masu neman ilimi, ina manufarka da iliminka? Ka tattauna a birnin zuciyarka. Idan kana cikin iyaye waɗanda suke da yara a sekondari ko kuwa a jami'a, ina dalilin da ka tura ɗanka a makarantar? Wace irin riba ce kake nema a wajensa nan gaba? Ko zai yiwu ku iyaye kun zama dalilin da 'ya'yanmu masu digiri sun dauki halin danniya domin kukan matsa su da karfi? Mai yiwuwa ne kai talaka, ka yi

sa'a har ɗanka ya sami digiri, kai kuma ka matsa shi har ya shiga aikin danniya. Wato ya yiwu talakawa da kansu sukan jawo ma kansu danniyar? Ko ya yiwu kai da kanka ka zama dalilin da aka yi maka danniya? Ka tattauna a zuciyarka da gaskiya.

MISALI 2 — Yadda masu ilimin zamani suke ƙin yin aiki a ƙauyuka ya zama abin damuwa. Wai kashi uku cikin huɗu na likitocin Nijeriya na zaune a Ikko (Lagos) da Ibadan. A halin da ake ciki dai injiniyoyi da sauran masu sana'a na zamani waɗanda ke ƙoƙarin kauce wa ayyuka a ƙauyuka sun yi yawa kwarai. Wato sukan ki su bauta ma mutanen da suka biya kuɗin makarantarsu ke nan!

TAMBAYA: Kai, talaka, mai yiwuwa ne ɗanka ne ke cikin waɗannan masu sana'ar zamani wanda ya ƙi aiki a ƙauye. Im ba kai ba, watakila ɗan wani baƙauyen. Ko ya yiwu kai, Babansa, ko ku kauyawa duka ku matsa ma yaranku masu ilimi irin wannan su zo su taimake ku a ƙauyenku? In su masu ilimin nan Kirista ne, mai yiwuwa ne ikilisiya ta matsa su su sa hannu cikin gyaran ƙauyenku komai sana'arsu. Ko kai, Babansa, kai da kanka ba ka so ya zauna a ƙauye domin ba zai sami zarafin cutar jama'a har ya kai ribar cutar zuwa gida ba?

MISALI 3: In mutum ya kai damuwarsa ga ofishin gwamnati ko na ƙaramar hukuma sau da yawa aka ba shi shawara cewa ya dawo gobe. Ba wuya ya gaji da tafiya ofishin gwamnati. Sai mutum ya bada toshiyar baki da ake bukata a gare shi ko kuwa ya bari ya huta ba tare da an biya masa bukatarsa ba.

TAMBAYA: Mai yiwuwa ne a ƙauyenku akwai irin wannan ofis inda aka ƙi biyan bukatar jama'a sai dai da wani abu a hannu. Ya kamata ku mutanen ƙauyen ku yi shawara tare ko da abin yi? In an nuna maku halin wurin,

me zai hana ku aika da wasu wakilan da za su zauna a ofis zuwa ran da za a biya bukatarku? Maimakon a je gida yad-da aka fadi, sai a zauna a ofishin a ƙi fita har lokacin da aka biya bukatar. Ko kuwa a je wajen ogansu a bayyana masa damuwarku. To, sai a yi shawara, amma kada a ce ba abin yi!

MISALI 4 — Da wuya talakawa ke biyan bukatar kansu da kuma da wuya za su sami hanyar ƙarin ribar amfanin gonakin-su, ba inda za su juya. Duk da haka dai su masu ilimin zamani suna karɓar albashi mai yawa, amma bai ishe su ba. Amma suna da hanya ko ta magana ko ta iko ma don a yi masu ƙari.

MISALI 5 — Ana gine-ginen gidaje masu tsadar gaske domin manyan mutanen gwamnati su yi zamansu a wurin a ƙebe, da dogayen hanyoyi masu kwalta, waɗanda ba su nufi ko'ina ba, sai dai wajen waɗannan gidaje. Daidai yadda ya faru a lokacin mulkin Turawa. A waɗannan kwanaki aka zuba kwalta a wata hanya cikin bani birni. Na tambayi wani mutum wanda ya san sha'anin gwamnati don shi da kansa ya taɓa zama kwamishina cewa me ya sa aka gyara hanyar da shi ke ba hanyar da jama'a masu yawa ke amfani da ita ba ce? Ya ce dalili shi ne akwai wasu manyan ma'aikatan gwamnatin jihar da ta tarayya waɗanda ke da gidaje a bakin titin. Akwai rashin hanyoyi da yawa a ƙauyuka har manoma ba su iya su kai amfanin gonarsu kasuwa ba, amma maimakon a gina marar kwalta mai araha sai aka kashe kudi masu yawa domin jin dadin manya. A wani wuri, ana kashe kudi masu yawa don gyaran hanya daga cikin gari zuwa filin jirgin sama. Har da mata masu shara. Amma in ka wuce filin jirgin sama kaɗan, sai ka ga an tsaida gyaran. Daga wurin sai paci-paci kawai aka yi.

Irin wannan danniya ba sabon abu ba ne a duniya. Ga abin da aka rubuta a Littafi Mai Tsarki a Yakubu 2:2-4, 6.

Misaɫi, in mutum mai zobban zinariya da tufafi masu ƙawa ya halarci taronku, wani gajiyyaye kuma ya shigo saye da tsummoki, sa'an nan kuka kula da mai tufafi masu ƙawan nan, har kuka ce masa, ''Ga mazauni mai ƙyau nan,'' gajiyayyen nan kuwa kuka ce masa, ''Tsaya daga can,'' ko kuwa, ''Zauna nan kasa gabana,'' ashe, ba ku nuna bambanci a tsakanninku ba ke nan, kuna zartar da hukunci da mugayen tunani? Amma kun wulakanta gajiyayyu! Ashe, ba masu arzikin ne ke matsa muku ba?

Talakawa ba kujeru ko riguna masu ƙawa suke nema daga gwamnati ba. Amma fa sai ka sake karatun waɗannan ayoyi amma inda ake zancen wurin zama sai ka sa zancen hanyar ka ga yadda ayan nan ta shafi zancen nan. Karatun zai fita kamar haka:

Misali, in mutum mai babban matsayi a gwamnati yana da gida a bakin wani titi a birni, waɗansu talakawa daga ƙauye kuma saye da tsummoki, sa'an nan kuka kula da mai babban matsayin nan, har kuka ce masa, ''Ga kwaltar da za mu zuba maka a gaban gidanka mai kyau nan,'' kuma ga yadda za a gyara maka hanya mai nisa har zuwa filin jirgin sama don kada ka sha kunya loton da waɗansu manya suka ziyarce ka ka kai su filin jirgin nan. Kuma ga 'yan kudi naira dubun dubbai don a shara maka hanyar '' Gajiyayyun nan kuwa kuka ce masu, ''Bi wancan hanyar daji da kafa,'' ko kuwa, ''Sai ka yi hankuri da rashin hanyan nan. Ba kudi yanzu. Muna kan shirin gina maku hanya. In kudi sun zo za mu yi maku hanya.'' Ashe, ba ku nuna bambamci a tsakaninku ba ke nan, kuna zartar da hukunci da mugayen tunani har kun hana talakawa kai amfanin gona kasuwa? Amma kun wulakanta gajiyayyu! Ashe, ba masu arzikin ne ke matsa muku ba? Ba su ne kuwa ke hana maku hanya da samun riba ba?

TAMBAYA: Donme ake yin haka? A ganinku ana taimakon wa a irin wannan hali? Ta haka aka kyautata zaman ƙasar Nijeriya kuwa? Halin nan ya nuna me ga talakawa? Ba reni ba? Ba danniya ba? Waɗansu masu irin wannan halin danniya Kirista ne kuwa! A ra'ayinka me ya sa suka yi haka? Ku jera dalilan irin wannan hali a gaban manya da kuma a gaban kanku, ku talakawa.

Babu shakka wasu manya sukan ɗauki irin wannan hali saboda rashin tunani da son kai. Sun ga haka akan yi da mulki; haka akan lura da manya da kuɗin jama'a. Su ma sun bi halin ba tare da wani tunani mai zurfi ba. An naɗe su da wani babban mukami ba tare da sun san wani abu akai ba. Sai suka bi halin da aka saba da shi kurum.

TAMBAYA: Ban da rashin tunani mai zurfi ba a rasa wasu dalilai na irin halin nan ba. Ku dinga tattauna zancen nan don a san dalilan duka. Kada a yi kyuyar tunani mai zurfi.

Bari a sa ku a hanya. Masu shirin irin waɗannan hanyoyin jin daɗin manya sukan rena talakawa.

TAMBAYA: Donme suka rena ku? Ina dallilin wannan?

Renin nan yana da wasu dalilai. Na daya masu iko sun manta yadda Allah Ubangiji ya halicce mu duka da surarsa a jikinmu, dukanmu, ba sai wasu kawai ba. Waɗansu cikin manyan nan Kirista ne, amma cikin nasu tunani suka raba zancen Bishara da na addini da sha'anin aikinsu. In ji su, sha'anin addini da na ruhaniya dabam; sha'anin aikin gwamnati da na kasuwanci dabam. Saboda haka surar da Allah ya halicci dukanmu da ita ba ta shafi irin wannan zance ba.

TAMBAYA: Me ya kamata a koya masu? Kuma wa zai koya masu ma'anar surar Allah? In kai makarancin takardan nan pasto ne, sai ka shiga tunani da zurfi kan haki naka cikin zancen nan. Ko ka taɓa yi wa wata koyarwa a

kai don a tsaida irin wannan reni? Ko kai da kanka kake da renin a zuciyarka?

Akwai kuma wasu dalilan renin nan a wajen mu talakawa.

TAMBAYA: Ina dalilan a wajenmu? Kada ku cigaba da karatu sai dai a yi tunani mai zurfi tukuna. Mu bincike kanmu mu sami wasu dalilai a wajenmu.

In an gama tattauna tambayan nan, a cigaba da karatu don a taimake mu cikin tunaninmu. Wani dalilin da ya sa ake yi mamu zamba shi ne TSORO. Mu talakawa muna jin tsoron manya. Su manya sun sani muna jin tsoronsu. Komai suka yi mamu, ba za mu ƙi ba. Kafin mu rabu da tsoron nan, muna bukatar karfafawa sosai daga cikin Littafi Mai Tsarki. Institute of Church and Society wadda ta wallafa littafin nan ta kuma buga wani littafi mai suna Kai da Dukiyarka. Littafin nan zai taimake ku don ku rabu da tsoron banza. Kuma Institute tana da ma'aikata wadanda za su iya zuwa su taimake ku akan batun tsoron nan. Sai ku yi kokari ku nemi littafin nan domin ku karanta Babi na Huɗu na littafin.

TAMBAYA: Me kuka gani batun maganar tsoron nan. Gaskiya ce kuwa? To, sai ku yi shawara tare da kuma ku karanta wancan littafi don ku san abin da Ubangiji Allah ke faɗi game da wannan batu.

Har yanzu fa ga wani dalilin da ya sa ake yi mamu zalunci. Wato manya sun sani mu talakawa ba masu haɗa kai ba ne. Sa'anda muke shan wahala, hada kai ya yi mamu wuya. Ba mu amince da juna ba, balle in haɗa kan ya shafi kuɗi. Mai yiwuwa ne kwanan baya kuna so ku hada kai don a gyara wani abu a kauyenku har kun tattara kudi, amma wanda aka danƙa masa kuɗi ya cinye ko kuwa wanda zai yi maku aiki ya cuce ku. Saboda haka haɗa kai ya yi maku wuya. Masu iko da manyan attajirai sun san mu da wannan hali na rashin hada kai da kuma haka suke so. Ba swa so mu haɗa kai ma domin cikin haɗa kai za mu sami karfi mu ƙi zaluncinsu. Sai dai bai kamata Kirista su

ƙi haɗa kai ba, domin tushen zaman Kirista haɗa kai ne, zumunta ce cikin sunan Isa Almasihu. A karanta 1 Korantiyawa 12:4-31 inda ake koya mamu cewa dukanmu gabobi ne na jiki ɗaya, wato na jikin Isa Almasihu. Kuma dukanmu muna da baiwa dabam dabam waɗanda za mu yi amfani da su don ginin jikin. To ɗayantakarmu ba ta shafi ƙungiyar da ake ce da ita ikilisiya kaɗai ba, amma ta shafe mu a kowane fannin zaman duniya. Ko za ku ce, "Mu talakawa ba mu da Ruhun Allah a zukatanmu?" Ke nan?

TAMBAYA: Mu tattauna ma'anar ɗayantakar Kirista cikin sha'anin shan tsananinmu da zamba. Yaya koyaswar Littafi Mai Tsarki za ta taimake mu cikin sha'anin? Muna da Ruhun Allah wanda zai iya mai da mu ɗaya don mu haɗa kai cikin kin zalunci da cuta ko ba mu da Ruhun? Sai a fadi gaskiya. Idan mun ce babu Ruhun Gaskiya a wajenmu, mun zama abin tausayi ke nan. Ya kamata mu roki Ubangiji Ya aiko mamu da wannan Ruhu.

MISALI 6 — Masu ilimin zamani suna da fahariya, suna ɓatad da kuɗaɗen da ke tsotse kuɗin harajin da talakawa suka biya ga gwamnati don gyaran ƙasa. Kirista ma na cikin wannan hali. Ana karfafa su su gwada wannan hali da bishara. Wani shugaban Kirista mai babban muƙami a gwamnati ya ce idan yana tafiya don aikinsa na gwamnati, yakan sauka cikin hotel mai tsada don kuɗin gwamnati ne, shi kuma babban mutum ne mai daraja wanda ya cancanta ya kashe kuɗi masu yawa. Amma sa'anda yake tafiya domin aikin ikilisiya, zai sauka a wuri mai araha domin ba ya so ya kashe kudin Ubangiji a banza. Ashe, akwai kuɗin gwamnati wanda ba na Ubangiji ba? Ai, 'yan'uwa, ba wani kuɗin da ba na Ubangiji ba, ko kuɗin gwamnati ko na kampani ko naka na kanka ko na ikilisiya: duk na Ubangiji ne.

TAMBAYA: Ina kuskuren masu ɓata da kuɗin gwamnati ko na kwamfani? Kuɗin wa suke ɓatarwa? A ganinka Allah na so manya su kashe kuɗinsa duka har ba sauran domin mu talakawa? Idan mun ga Kirista na ɓatar da

kuɗin gwamnati ko kuwa kayan gwamnati a banza me ya kamata a yi masa? A tuna da hanyar da Ubangiji ya koya mamu a Mat. 18! Ana aiki da hanyar a wajenku kuwa? Im babu, me ya hana?

## C. ZALUNCI A CIKIN TSARIN GWAMNATI

Gwamnati akai akai takan yi shirye-shirye waɗanda da niyyar su zama da amfani ga jama'a baki ɗaya. Amma ba da daɗewa ba ma'aikata masu wayo suka koyi hanyoyin da ba su wajaba ba, domin a zambaci talakawa.

MISALI — Kowane manomi ya san wuyar samun takin zamani daga wuraren da aka kakkafa domin samun takin. Kada ma a yi magana akan motar noma ta gwamnati ko samun allurar rigakafin ciwon kaji daga hukumar lafiyar dabbobi. In ba da wani abu a hannu ba, to, dai...

TAMBAYA: Idan an kafa ayyuka irin waɗannan a wajenku, amma ba ku samun amfaninsu, babu abin yi ke nan? A yi shawara. Cikin shawarar dai kada a manta da ayoyin da aka kawo a baya. Kuma a tuna da Babi na 4 na cikin littafi mai suna Kai da Dukiyarka.

MISALI 2: Rance iri dabam-dabam na gwamnati don inganta noma ba a kimanta su daidai bisa ga bukatar manoma. Dalilai biyu ne: (a) Ana bukata a cika waɗansu fom waɗanda aka rubuta su a cikin dogon Turanci mai zurfi. (b) Yadda hanyar samun rancen take, ba shi yiwuwa talakawa su samu. su ne kuwa mutanen da suke da bukatar rancen.

TAMBAYA: Babu shakka manomi ɗaya ba zai iya magance damuwar ba, amma idan an hada kai fa? Ina hanyar da za mu bi don mu sami rabonmu cikin waɗannan rance?

Amma dai ran wanka ba a ɓoye cibiya. Daya cikin dalilin da suka sa bankuna ke kin ba da rance ga talakawa shi ne, wato sau da yawa mai ƙarbar rancen ba zai yi amfani da rancen don ya inganta noma ba, amma zai kashe kuɗin wajen ƙara mata ko sayen mota. Kuma akan kasa mayar da kuɗin rancen cikin lokacin da ya kamata. Ya kamata mu talakawa mu nuna ma bankuna cewa mu masu gaskiya ne; za mu yi aiki da kudin domin ingantar noma don in lokaci ya yi mu mayar bisa ga alkawarin da muka yi.

TAMBAYA: Ko akwai manoma a wajenmu waɗanda suka ƙarbi rance amma suka batar da kuɗin ta wata hanyar da ba ta kamata ba da kuma ba a mayar cikin lokaci ba? Sai a faɗi gaskiya. In akwai irin wannan mutum a cikinmu bari ya sani cewa shi ne dalilin da sauranmu ba mu iya samun rancen ba.

MISALI 3—Rashin samun magunguna a asibitan gwamnati da ɗakunan magani ƙauyuka gaba ɗaya, talakawa sun gaji da shi. Bugu da kari, ga kuma toshiyar baki wanda ya zama tilas ka bayar kafin a lura da kai a ba ka magani a cikin waɗansu asibitai. A Institute of Church and Society muna da wani ma'aikaci wanda sana'arsa ita ce kiwon kaji. Amma bai sami wata riba ba domin yawan toshiyar da ma'aikatan hukumar lafiyar dabbobi ke nema a wajensa har ya bar sana'a kiwon kaji saboda zambar ta fi ƙarfinsa.

TAMBAYA: Jama'a ya kamata mu dinga hakuri da halin nan ko kuwa da abin da za a iya yi cikin haɗa kai? Me zai hana inda ake fama da wannan damuwa a je wajen offishin mutanen nan a nuna masu laifinsu ba da tsoro ba? Idan akwai Kirista cikin ofis din, me za a iya yi da shi ko kuwa ita?

MISALI 4: Me ya faru da ribar da ake samun daga wajen hukumomin da gwamnati ta kakkafa don sayen amfanin gona? Masu ilimin tattalin arziki sun ce akan ɓata ribar ta hanyar da ba ta kamata ba. Waɗansu akan ɓata ta hanyar banza kurum.

Sauran akan yi amfani da su don inganta zaman birane. Ga shi kuwa wannan riba ta samu ne ta wajen manoman da ke ƙauyuka, amma ana amfani da ƙudin don birane! Har ila yau, ga naira zambar dubbai da ake ɓatarwa wajen kwangila masu tsadan nan.

MISALI 5— Da alama cewa ƙananan hukumomi ba wani abu ba ne, sai dai iko kawai na fahariya ga kansiloli. Ya kamata a yi waɗansu shirye-shiryen da za a sa kansiloli na ƙananan hukumomi su gane dabaru na gaskiya wadanda kowa zai sami rabo a cikin hukumomin baki ɗaya.

> TAMBAYA: Idan a wajenku an ga waɗansu kansiloli na neman cingaban kansu fiye da na jama'a, ina maganin da za a yi masu cikin haɗa kai? Ku jera wasu abubuwan da za a iya yi masu don su rabu da halin nan.

Duk da haka dai babu dalilin da talakawa za su dinga yarda da wannan zalunci da kuma hanƙuri. Bishara wani iko ne wanda yakan 'yantad da tunanin mutum. Bishara iko ne wanda ya kamata mu Kirista mu yi amfanin da shi, mu yi wa'azinta don 'yantad da talakawa kuma don a ga amfanin bishara ta Isa Almasihu. Amma ana ganin waɗansu Kirista masu ilimin zamani suna haɗa kai da masu yin tsanani da zambar, waɗansu kuma sun yarda da tsananin cikin hanƙuri cewa kaddara ce. Dole ne dukansu su kasa kunne a ga Bishara, su sake tunaninsu, su kuma gane gaskiyar aikinsu a gaban Ubangiji Allah.

Talakawa, kada a fid da zuciya, amma a tuna da bayyanin da Yesu ya yi a Luka 4:18. Duba shafi mai lamba 8 a baya.

Mu Kirista masu ilimi da masu iko mu kasa kunne ga jawabin waɗannan ayoyi daga cikin Littafi Mai Tsarki:

La antace ne shi wanda ya ƙwace ma baƙo shari'a, ko maraya, ko gwamruwa (K. Sh. 27:19).

Wanda ya toshe kunnuwansa ga jin kukar talaka, shi kuma zai yi kuka, ba kuwa za a ji shi ba (Mis. 21:13).

Kaitonsa shi wanda ya gina gidansa ta wurin rashin adilci, ɗakunansu kuma da zamba, wanda ya mori aikin ɗanuwansa ban da lada, ba ya ba shi hakinsa ba. Ya ce, zan gina babban gida... (Irm. 22:13-17).

Kaiton waɗannan da suka tuna dabarar zamba, suna aika mugunta a bisa gidajensu! Lokacin da gari ya waye sukan aikata shi domin yana cikin ikon hannunsu. Su kan yi ƙyashin gonaki, su ƙwace su kuma; gidaje kuma, har su amshe su; su kan zalunci mutum da gidansa, i, har mutum da gadonsa (Mikah 2:1-2).

Bari kuma a karanta waɗannan ayoyi domin a gane cewa lalle Ubangiji yana da wata ƙauna ta musamman domin talakawa. Kuma Ubangiji baya karɓar aikin addini na mutum wanda ke zaluntar 'yanuwansa.

K. Sh. 10:18
Zab. 33:5
Mis. 14:31
Mis. 17:5
Mis. 22:22-23
Ish. 11:1, 4-5
Ish. 25:4
Ish. 41:17
Ish. 61:8
Eze. 34:16
Fit. 22:21-22
Lev. 19:15
K. Sh. 27:19
Mis. 21:13
Mis. 22:9

Mis. 31:8-9
Mis. 24:11-12
Mis. 28:27
Mis. 29:7
Ish. 3:14-15
Ish. 10:1-3
Ish. 56:1
Ish. 32:6-7
Ish. 58:10
Irm. 7:6-7
Irm. 21:12
Irm. 22:3
Eze. 16:49
Eze. 18:59, 16-17

Eze. 45:9
Dan. 4:27
Hos. 12:6
Amos 1:9
Amos 2:6-7
Amos 4:1-2
Amos 5:15
Amos 8:4-7
Mikah 3:1-3
Mikah 6:8
Mikah 6:10-12
Hab. 2:6
Zech. 7:9-10
Amos 5:21-24

Mat. 5:3-6
Luka 6:20-21
Mat. 18:1-4
Mat. 20:25-27
Luka 22:24-27
Luka 16:15
Yak. 4:6-10
Yoh. 12:25
Wa. Yoh. 2:10
Fil. 2:5-11
Mat. 10:38-39
Mat. 16:24-25
Mk. 8:34-35

A.M. 14:22
2 Tim. 1:18
2 Tim. 2:3
Af. 4:22-24
Mt. 7:12
Lk. 6:31, 35, 38
Mat. 22:37-40
Yoh. 15:12-13
Rom. 13:9-10
1 Kor. 10:24, 33
Gal. 6:10
1 Yoh. 2:15-16

1 Yoh. 4:21
Mat. 9:13
Lk. 14:12-14
A.M. 20:35
1 Kor. 5:11
Gal. 6:9-10
1 Tim. 6:9-17
2 Tim. 3:1-4
Ibran. 13:5
Yak. 1:27
Yak. 2:1-7
Yak. 5:1-6
1 Yoh. 3:16

Waɗannan ayoyi duka za a same su cikin Littafi Mai Tsarki da kuma cikin littafi mai suna Kai da Dukiyarka. Sai ka nemi littafin domin ka same su ayoyin ta hanya mai sauƙi.

WANDA YA KARANTA WAƊANNAN AYOYI ZAI GANE CEWA ALLAH YA KI CUTA DA DANNIYA DA ZALUNCI DA KETA DUKA. BA WANI DALILIN DA ZA A CE, "AI, KADDARAR ALLAH CE." A GANE CEWA ALLAH NA TARE DA TALAKAWA, YANA KAUNARSU. RANAR FANSA TA KUSA. BARI MANOMA SU ZAƁI IRIN GWAMNATIN DA ZA TA YI AIKI DOMIN ADILCI YA TABBATA. YA KAMATA MANOMA SU NUNA RASHIN YARDARSU SA'ANDA SUN GA AN AIKATA MUGUNTA. BARI SU KAFA KUNGIYOYIN MANOMA WAƊANDA ZA SU YI SHAWARA GAME DA WAƊANNAN BATUTUWA WAƊANDA KUMA SU IYA RIBATO MASU AMFANI NA GASKIYA DOMIN DUKANMU.

## IKILISIYA MATAIMAKAN TALAKAWA

Sashen da muka wuce yanzu ya bayyana cewa sai ka ce ba abin da ake yi wa talakawa sai zalunci. A zahirin gaskiya dai, waɗansu manya cikin gwamnati da kuma cikin ikilisiya na ƙoƙari matuƙa domin a ƙyautata zaman jin daɗin rayuwarsu. Waɗansu na taimakon talakawa ba kaɗan ba. Waɗansu kuwa suna ƙoƙarin taimako, amma saboda rashin ganewarsu ƙoƙarinsu ya kasa, bai kai su ko'ina ba. Tun da shirinmu shiri ne na ma'aikatan ikilisiya bari mu taƙaita irin ayyukan da ikilisiya ta kafa don inganta zaman ƙauye.

### A. CINGABA A AIKIN MAGANI

1. Yawancin ikilisiyai a ƙasar Nijeriya sun kafa hukumomi domin kyauta cin gaba a aikin asibiti duka da kiwon lafiya. Ban da su manyan asibitocin da ikilisiyai suka gina cikin garuruwa ga

kuma kan'anan ɗakunan magani da ɗakunan haifuwa cikin ƙauyuka masu ɗimbin yawa. Sau da yawa 'yan ƙasa suka hada gwiwarsu da ikilisiya don ginin waɗannan ɗakunan. Ikilisiya takan ba su ma'aikata da kuma magunguna.

2. Akwai kuma shirye-shirye aikin asibiti da ke zirga-zirga, ana kewayawa akai akai, domin bada magungunan rigakafi, su bada shawarwari ga mata masu juna biyu da kuma lura da 'ya'yansu. Kuma sukan koyar da hanyoyin kiwon lafiya.

3. Inda babu ɗakin magani wasu ɗariku sukan shirya dabarar aikawa da masu ba da taimako na farko wanda da Turanci ake ce da shi "first aid." Ikilisiya takan koyar da aikin nan da mutanen ƙauyensu kansu. Akan yi masu kos na wajen wata uku. In an ga ƙoƙarinsu kuma, sai a ƙara masu koyarwa har sun zama masu ba da magani sosai. Za a kuma ƙara darajar aikin magani har ya zama kamar ɗakin magani na musamman.

4. Hukumomin kiwon lafiyar jama'a na ikilisiyai sun haɗa kai domin su rage wahalar neman magunguna kuma a rage kuɗin magunguna don kada tsadarsu ta fi karfin talakawa. Ga Christian Central Pharmacy (CCP) a Jos inda wasu ɗarikai a nan Nijeriya ta arewa ke samun magungunansu da araha. Daga baya kuma wata hada gwiwar manyan dariku daga ko'ina cikin Nijeriya mai suna Christian Health Association of Nigeria (CHAN to kuwa Majalisar Kirista ta Kiwon Lafiyar Jama'a a Nijeriya) suka kafa wata ƙungiya mai suna Champharm a Jos. Yanzu ikilisiya tana taimakon talakawa da magani mafi araha ta wurin waɗannan wurare guda biyu. Kuma waɗannan wurare guda biyu na shirin hada magani a nan Nijeriya don kada a dinga hulda da ƙasashen wajen don samun magani.

5. Waɗansu ikilisiyai kuma suna ƙoƙari su horad da masu sana'ar aikin jinya da kuma na gwada jini da masu ba da magani a ƙauyuka. Misali: Mkar Christian Hospital a Jihar Binuwai da kuma ga Church of Christ in Central Nigeria (CCCN) a Akwanga a Jihar Pilato.

6. Kada kuma a manta da aikin da ake yi ma kuture a inda ake warkad da su kuture akan kuma koya masu aiki irin dabam dabam da za su iya yi ko da yake sun rasa yatsa ko hannu ko ƙafa. Misali, Mangu Leprosy and Rehabilitation Centre na COCIN a Jihar Pilator da kuma wani aikin da su NKST suka kafa kusa da Mkar a Jihar Binuwai.

7. An riga an ambaci Christian Health Association of Nigeria ko kuwa CHAN. Ban da kawo magunguna da araha daga ƙasashen waje, ita ƙungiyar kuma ta dauki shugabanci cikin waɗansu fannonin da suka shafi lafiyar jama'a. CHAN ta kafa wata hukumar da ake ce da ita Hukumar Primary Health Care, wato sukan inganta aikin magani a ƙauyuka ko'ina a Nijeriya. CHAN ta ga akan kashe kuɗi da yawa kan asibitocci, amma talakawa da sauran mutanen kauyuka ba su samun amfanin waɗannan asibitoci. Yanzu CHAN na ƙoƙari ta inganta aikin magani a ƙauyuka, musamman zancen rigakafi har Hukumar Lafiyar Jama'a ta Gwamnatin Tarayya na neman shawara daga wurin CHAN domin ba wadanda suka fi CHAN ganewa cikin aikin magani a ƙauyuka. Kuma CHAN ta kafa wata hukuma mai suna Wholistic Health Care Project wadda ke ƙoƙari ta jawo hankalin masu aikin jiyya cewa idan ana so a warkad da mara lafiya ya kamata a tattauna tushen ciwon da ke damun shi, kada a tsaya a maganin ƙwaya ko kuwa na allura. Idan am ba mutum maganin ciwon kai amma ba a tattauna dalilin da ciwon nan ya same shi ba, ai, ciwon ba zai warke ba. Ina dalilin da ya sa aka sami ciwon nan? A nemi dalili kuma a yi maganinsa.

Abubuwan da ke aukuwa a wurin waɗannan harkokin aikin asibiti sun wuce a auna su. Mai yiwuwa ne a yi lissafin marasa lafiyar da suka warke, amma ba dama a gwada murnarsu ta warkewa.

## B. CINGABA A AIKIN GONA

Yawancin ɗariku sun kakkafa ƙungiyoyin aikin gona da manufar su inganta zaman rayuwar manoma. Su ƙungiyoyin

nan sun yi yawa kamar su:

Faith and Farm — COCIN a Vom, Jihar Pilato
Kyautata Zaman Kauye — ECWA, a Jos
Christian Rural Development — Christian Reformed Church of Nigeria a Mararaba, Karamar Hukumar Donga, Jihar Gongola
Christian Farmers'-Association — Anglican a Kafanchan,, Jihar Kaduna.

Daidai da hukumomi masu inganta aikin jiyya na ɗarikan ikilisiya haka masu inganta aikin noma suka kafa nasu haɗa gwiwa. Ga Christian Rural Advisory Council (CRAC) da kuma Christian Rural Fellowship of Nigeria (CRFN). Cikin waɗannan hukumomin masu inganta aikin noma sukan yi shawara da juna kuma su taimaki juna. Marigayi Mallam Joseph Jibi ne ɗaya daga cikin masu kafa waɗannan hukumomi. Bai kamata a manta da shi ba.

Waɗannan ƙungiyoyin noma na ikilisiya na yin hidimomi iri-iri. Suka kawo magungunan aikin gona, sukan koyar da sababbin hanyoyin shuki da lura da shuke-shuke. Sukan kawo sabon iri da kuma 'yan tsaki har ma sukan kawo kuɗi domin a ba manoma rance. Kuma sukan kakkafa ƙungiyoyin manoma inda su manoman suke aiki tare da shawara.

Sakamakon waɗannan harkoki ya zama da amfani ƙwarai da gaske da shi ke manoma sun ribato sababbin hanyoyin amfanin gona har sun sami amfanin gona fiye da da. Yanzu ana ganin bukatar samun kaji ƙwarai. Kuma waɗansu sun soma gane gaskiyar amfani adana su domin hana cuta. Waɗansu sun koyi yadda ake amfani da magunguna da kuma hanyar ajiyar amfanin gona. Muhimmancin waɗannan ƙoƙari yana da wuya a kimanta a matsayin da kayayyaki da ƙyar suke samuwa. Waɗannan shirye-shiryen sun farkar da jama'a, waɗansu kayayyaki kamar su wayar kaji da magunguna har 'yan kasuwa na kawowa su sayar. Wato yanzu ana iya samunsu a kasuwa. Yanzu manoma ba su dogara ga ƙungiyoyin nan domin biyan bukatarsu, amma suna dogara ga 'yan kasuwa kuma. Waɗansu

manoma sun iya ɗaura auren itatuwan lemo har kuma su sayar da su. Ba shi yiwuwa a kimanta irin sakewar hankalin mutum. Yadda manoma ke yin amfani da sababbin hanyoyin noma ma babbar nasara ce wadda ba dama a kimanta ta a dan littafin nan.

Ban da irin waɗannan ƙungiyoyi kuwa ikilisiyai na koyar da noma cikin makarantarsu ta Littafi Mai Tsarki domin shugabannin ikilisiya su san noman zamani kuma su koya ma jama'asu. Makarantar da ke ɗaukar nauyin wannan aiki musamma ita ce Kulp Bible School a Ikilisiyar 'Yan'uwa A Nijeriya kusa da Mubi, Jihar Gongola, wato E.Y.N.

## C. BUKATA DOMIN KARIN FADAKAR DA MANOMA

Ɗan Agbese yana ɗaya daga cikin ƙungiyar da ta kafa wata jarida mai farin jini a kasar Nijeriya mai suna Newswatch wadda kwanan baya aka kashe babban editansu, wato Dele Giwa: Shi Ɗan Agbese din da edita ne na jarida mai suna Standard wadda ake wallafa ta a Jos. To, mutumin nan ya rubuta waɗansu bayyanai masu nauyi ƙawarai da gaske cikin jaridar Standard a ranar 14 ga watan Yuli a shekara ta 1978 batun talakawa. Ya rubuta cewa mutane da dama suna yin hidima ta wurin taimakon talakawa, amma wahalarsu talakawan ba ta taɓa kyautatuwa ba. Ko ɗa ya ke wasu na iyakar ƙoƙarin su inganta zamansu, duk da haka har a yau suna cikin talauci. Ya cigaba da cewa:

> Talaka mai hanƙuri ne. She mai jurewa ne. She dai mai gafartawa ne gaba ɗaya. Bai taba nuna rashin yarda ba. Bai taɓa faɗa don amfani da jin daɗin kansa ba in dai akwai wadanda za su yi dukan fadan dominsa. Ana moransa ne; ana cin mutumcinsa...

Mallam Labaran, edita na wannan Littafi, ya kara bayyanai da cewa "Talaka bawa ne, sai an buga ake tayarsa."

Wato Ɗan Agbese ya bayyana halin kaddara ke nan. Ba wai muna so mu ƙasƙantar da hidimomin ƙungiyoyin magani da na noma da aka taƙaita su a baya ba. Amma an nanata cewa wajibi

ne a kawar da wannan mugun hankuri da jurewa. Loto-loto su kungiyoyin magani da na noma na kokarin yin haka. Misali wani wuri idan manoma suka sayar da amfanin gonakinsu da araha. Marigayi Joseph Jibi ya zo ya hada manoman don ya ba su shawara cewa su yi tsarin kungiyarsu don baki daya kowa ya ki sayar da nasa hatsi da araha. Su 'yan kasuwa masu wayo wadanda suka saba su kwashe amfanin wadannan manoma da araha sun rasa abin yi. Sun zo suna rokon Mallam Jibi su kawar da zartarwar da suka yi, amma ba su ci nasara ba. An kafa sharudda wadanda suka zama dole 'yan kasuwan nan su yarda da farashin amfanin gona da ya dace. A nan ne fa manoman sun samin cin nasara.

Abin tausayi ne. Su manoman ba su cigaba da irin wannan shirin cikin shekaru gaba ba da kuma ba a gwada halin nan cikin wadansu kauyuka ba. Amma saboda abin da ya aukun nan mun ga wani tushe na irin cingaban da ake bukata wajen manoma. Ikilisiya tana koyar da biyayya; kungiyoyinta sukan kyautata aikin noma, amma ba wanda ya taba nemo hanyar tattara hankalin manoma domin su yi shawara da juna yadda za su daga da yin magana akan abin da shi ke hakkinsu ne.

Bari ikilisiya da kungiyoyinta cikin wa'azinsu da kuma cikin koyarwarsu su kawar da kuskuren masu bi batun kaddara, a koya masu tushen bangaskiya ta Kirista wanda zai 'yantad da manoma a raba su ta tsoronsu da irin wannan hankuri na banza. Wani karin magana ya ce "Kada a yi hakuri da ciwo da talauci." Bishara wani IKO ne, amma ba a gane ma'anar ikon sosai ba. Almasihu ya zo don kawo saki, kuma don ya KAKKARYA KARFIN MASU NUNA IKO DA WAYO DA ZAMBA. Amma an mai da wannan batu sai ka ce ya shafi zancen ruhaniya ne kadai, bai shafi zamanmu a duniya ba.

A ranar saukowar Ruhu Mai Tsarki, wato ranar Fentikos a Ayyukan Mazanni 2:17 zuwa gaba, Bitrus Manzo ya bayyan cewa Ruhun nan zai kawo wani sabon hali, sabon tunani, sabon bege cikin zukatan jama'a masu bin Almasihu. Manya da yara, maza da mata har da bayi ma za su gaji wani hali da kuma wani

bege har a kawar masu da tsoro a zukatansu. To, babɓan begen da aka sa a zukatansu shi ne begen sabuntuwar duniya da ta sama duka don a kafa gaskiya da adalci a duniya inda babu hawaye, ba azaba. Karanta Babi na 6 na cikin littafin Kai da Dukiyarka don ka gane da irin duniyar da mu Kirista muke begenta.

Littafin kuma ya koya mamu cewa mu 'yan adam ba za mu iya kafa irin wannan sabuwar duniya da ikon kanmu ba. Kuma ba za ta kafu ba ma sai dai ta wurin Isa Almasihu a lokacin dawowarsa. Duk da haka dai dole ne begen nan TUN YANZU A CIKIN NAMU ZAMANI NA YAU ya zama jagorarmu. Saboda begen nan za mu kawar da tsoronmu da ƙyuyarmu tun yanzu. A kashin gaskiya ikilisiya ba ta ɗaga kan wannan koyarwar da ke cikin Littafi Mai Tsarki ba. Ikilisiya na nanata zancen hanƙuri da cewa ladarmu a same take. Lokaci ya yi mu kasa kunne ga Yakubu wanda ya rubuta cewa, "A kan misalin shan wuya da haƙuri kuma, 'yan'uwa, ku dubi annabawa ma da suka yi magana da sunan Ubangiji" (Yakubu 5:10). Don ka gane irin maganganun da su annabawa na da suka yi cikin sunan Ubangiji ka tuna da karatun da ka yi cikin Babi na 4 cikin Kai da Dukiyarka. Kuma ka sake karanta ayoyin da aka buga a baya shafi 23.

Yanzu ga tambayoyi zuwa gareku manoma da kuma gareku ƙungiyoyin inganta aikin jiyya da noma: Ta yaya ku talakawa za ku ɗauki wannan sabon begen nan da sabon halin wanda Ruhun Allah ke shiryawa dominku har ya shiga cikin birnin zukatanku ku yi aiki da shi? Ta yaya ku Kirista talakawa za ku tsaya da karfin da Allah ya tanada maku ta wurin Isa Almasihu da kuma ta wurin Ruhunsa Mai Tsarki? Me ya sa ba ku yin aikin da irin wannan begen da sabon halin? Ina dalilin tsoronku? Yaushe za ku haɗa kanku har masu aikin gwamnati masu kawo magani da taki su san darajarku su ji tsoronku har su kawo abin da ke naku?